**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**

A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)

**DOI:** https://doi.org/10.65760/kassu.i1.1 **Website:** www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Tauri A Farfajiyar Tunanin Abubakar Kassu Zurmi

**Abubakar Sani Sayaya**
**Iyatanci Kofar Sauri Katsina**

**Corresponding Author: Abubakar Sani Sayaya** asanisayaya@gmail.com

**Tsakure.**

*An yi wa wannan takardar take da “* ***Tauri A Farfajiyar Tunanin Abubakar Kassu Zurmi”.*** *An Gina ta ne da nufin fito da irin fashin baƙin da Abubakar Kassu Zurmi ya yi wa al’adar Tauri a cikin waƙoƙinsa. Takardar an ginata ne ta hanyar nazartar wasu muhimman aiyukan da aka wallafa da waɗanda ba a wallafa ba. Haka kuma an nazarci wasu turakun waƙoƙin da Kassun ya gabatar, musamman waɗanda suke magana a kan Tauri da magungunan Tauri. Ganin cewa Kassu Zurmi ya naƙalci al’adar Tauri ya sa aka ɗora wannan aiki a kan Karin maganar Hausawa da ake cewa* ***“Masu abi su ke da abinsu”.*** *An yi tsokaci ne a kan irin fashin baƙin da Kassun ya yi wa al’adar Tauri acikin sassa guda uku. A sashe na farko an yi tsokaci a kan ma’anar kalmomin da suka haɗa da* ***Tauri*** *da* ***Farfajiya*** *da kuma* ***Tunani*** *tare da bibiyar ire-iren magungunan da ‘yan tauri ke amfani da su, da wasu kalmomi da Kassu ya yi amfani da su a mamadin maganin tauri da kuma yadda ake amfani da magungunan. Sashe na biyu an yi tsokaci ne a kan irin hangen da Kassu ya yi wa al’adar tauri. A sashe na uku an gabatar da shawarwari da ake ganin sun dace. An gabatar da sawarwarin ne ta hanyar tuntuɓar wasu turakun waƙoƙin shi Kassu Zurmi ɗin. Sakamakon da aka samu yayin gina wannan takaarda ya tabbatar da cewa makaɗa Kassu Zurmi ya taskace al’adar tauri kafin rasuwarsa.*

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

A cikin kowace al’uma, kuma a lokutta mababanta akan samu ɗaiɗaikun mutane da kan yi fice a ɓangaren rayuwa da suka sa gaba. Ire-iren waɗannan mutane, rayuwarsu ta kan

kasance abin alfahari ga al'umarsu. Wasu ana sanin muhimmancinsu a irin ficen da suka yi tun suna raye wasu sai bayan mutuwarsu ake fahimtar muhimmancin su a cikin al'uma. Ire-iren waɗannan mutane sun kasance waɗanda ke ba da gudummuwa ga ci gaban rayuwa ta hanyar amfani da irin fasahar da Allah Ya ba su. Irin wannan gudummuwa da suka ba da kan sa a riƙa tunawa da su, ko da ba su raye. Daga cikin wannan al'uma tamu ne, Allah maɗaukakin Sarki Ya samar da wannan mashahurin mawaƙi. Alhaji Abubakar Muhammadu Kassu Zurmi, wanda ya shahara a fannin waƙoƙin maza da suka haɗa da waƙoƙin Faruta da na Tauri da kuma na Sata.

Ganin yadda al'adat Tauri ta kasance ɗaya daga cikin manyan sassan da Kassu Zurmi ya gina waƙoƙinsa ya jaza gudanar da wannan aiki domin a gano yadda al'adar ta ke daga bakin masana. Wato a gano tare da fito da fasalin Tauri, kamar yadda Kassu Zurmi ya fito da su a cikin waƙoƙinsa, da irin gudummuwar da ya bayar wurin taskace waɗannan al'adu. Domin ganin an samu ingantaccen sakamo za kasa aikin zuwa sassa uku. A sashe na farko za a yi tsokaci a kan tarihn rayuwar Makaɗa Kassu Zurmi da Tauri da magunguna Tauri. A sashe na biyu za a fito da irin hangen da Kassu Zurmi ya yiwa al'adar Tauri sannan a sashe na uku za a gabatar da shawarwarin da ake ganin sun dace.

**2-1 Tarihin Abubakar Kassu Zurmi**

Wani makaɗin Farauta mai suna Gandau, wanda asalinsa Bagobiri ne da ya taso daga wani gari da ake kira Kurawa a ƙasar Gobir tare da ɗansa Muhammadu. Kassu Zurmi ya tabbatar da kasancewarsu mutanen Kurawa a cikin waƙar da ya rera wa Ummaru Sanda Bagobiri, inda ya ke cewa:

*"A! Rad da Allah Yay yo ni,*
*Kassu rad da Mai sama Yay yo ni,*
*Ka ga dan nan ban zo kiɗi ba Sabon-birni,*
*Sai da Ummaru yai kiran mu sabon sarki,*
*...............................................................*
*Sai da Ummaru yai kiranmu sarki naz zo,*
*Amma in baccin rashin sani,*
*Ba baƙo ba ne gida nid dawo,*
*Gida Kurawa"*.

Bayan rasuwar Gandau sai mahaifin Kassu da ake kira Muhammadu ya tashi daga garin Dumfawa ya koma Magarya a masarautar Zurmi, kuma a nan ne aka haifi Abubakar Kassu Zurmi. Ana hasashen cewa an haifi makaɗa Abubakar a cikin shekara ta dubu da ɗari tara da goma sha huɗu (1914). A cikin wanan shekarar ne Allah Ya albarkaci Muhammadu da samun haihuwar ɗa namiji da aka raɗa wa suna Abubakar. An haifi Abubakar a ranar kasuwa, dan haka sai aka yi masa laƙabi da MaiKassuwa. Sunan da ya bi Abubakar har aka kai fagen da ya sauya zuwa Kassu. Daga bisani Muhammadu wato mahaifin Kassu ya tashi daga Magarya ya koma Kadawa. Sakamakon waɗansu dalilai Muhammadu sai ya sake dawowa Magarya da zama, amma a lokacin shi Kassu sai ya yi zamansa a Kadawa tare da ƙanen mahaifinsa mai suna Abdullahi. A nan ma Kassu ya jaddada kasancewarsa mazaunin garin Kadawa a cikin waƙar Nomau na Magarya. Yana cewa:

*"Uban Balindu shi yai isheni hak Kadawa,*
*Ya ce Kassu ana biɗak ka da doki gashi kana alfarma".*

Ko da yake Muhammadu, wato mahaifin Abubakar Kassu Zurmi makarancin Al'ƙura'an ne, hakan bai hana shi kiɗin Farauta ba, wanda ya yi da ganga. Wannan ne ya sa

shi ma ɗan nasa, wato Abubakar Kassu Zurmi ya yi gadon kiɗan farauta. Kassu ya fara bin mahaifinsa wajen kiɗan farauta tun yana yaro ƙarami, ya fara kiɗin farauta da ganaga kafin daga bisani ya koma amfani da kalangu. Waƙoƙin da ya fara rerawa da ganga sun haɗa da waƙar Sarki Bahago da ta Labbo Katakare da waƙar Gandau waɗanda daga baya ya mayar da su da kiɗan kalangu. Waƙar farko da ya fara da kiɗan kalangu ita ce ta Namande uban tafiya, wato Garu-garu. Kassun ya tabbatar da hakan a cikin waƙar ta Garu-garu kamar haka:

*"Hwarautad da mun ka je dajin Rayya,*
*Shi yac ce in tahi da kalangaina,*
*Nac ce ma shi ba ni zuwa,*
*Dan hwa ka sa in take uwayena,*
*Yac ce in da tahi ba komi".*

Kamar yadda Gusau, (2011) ya bayyana cewa "Kassu Zurmi kiɗan farauta ya gada, ya taras ubansa yana yi, don haka, ya himmatu a kansa, har Allah Ya ba shi rabo mai yawa a ciki". Mawaƙin ya tabbatar da irin shaharar da ya yi a fagen waƙoƙin 'yan tauri da na farauta. Ya kuma tabbatar da hakan ne a cikin waƙar Basare Ɗan'isiyaku na Nomau. A cikin yana cewa:

*"Yan tauri ku riƙe ni gaskiyar Allah,*
*Tunda Kassu yanzu na zam matat tsara,*
*A'a ka miji ba ya sonmu sai ran taron kunya,*

Kassu Zurmi ya yi karatun Al'ƙur'ani a wurin mahaifinsa da kuma wasu malamai da ke kusa. Wannan ne ma ya sa har yanzu akwai makaranta Al'ƙur'ani a cikin ɗiyan nasa. Allah Ya albarkaci Kassu Zurmi da samun haihuwa ta ɗiya maza da mata guda goma. Daga cikin ɗiyansa maza akwai: Ummaru ƙaho da Sani Ɗangabci da Malam Ango da Ali Namakka da kuma Rabe. Ummaru Kaho da Sani Ɗangabci su suka gaji kiɗan Tauri daga wurin mahaifin nasu.

## 1.2 Ma'anar Kalmar Tauri

Kalmar Tauri, kalma ce wadda da yawa suna ganin ta samo asali ne daga Bahaushiyar kalmar nan ta 'Tauri' wadda ke gwada cewa wani abu mai ƙarfin gaske wanda kafin a sarrafa shi sai an sha wuya. Daga wannan ma'ana ce aka ba wannan kalmar ta Tauri wadda wata hanya ce da Bahaushe ka bi domin ya mayar da jikinsa mai gagarar duk wani makami da ka iya fasa shi. Masana da yawa sun tofa albarkacin bakinsu danagane da ma'anar kalmar ta "Tauri". Sayaya (2019:23) a ƙoƙarinsa na fito da ma'anar kalmar Tauri, cewa ya yi:

> "Tauri wata hanya ce da Hausawa ke amfani da wasu sinadarai da ake samu daga wasu itatuwa ko tsirrai, ko sassan jikin wasu halittu, misali kwari ko dabbobi su sarrafa su ta hanyoyi daban-daban, domin samun kariya daga rauni ko cutarwar da wani makami ka iya yi ma su. Iri wannan kariya da jiki ke samu, shi ake kira "Tauri". Duk wanda ya ci maganin tauri ya kama masa jiki shi ake kira "Ɗan tauri". Ko "Yan tauri", (jam'i).

Su 'yan tauri su ne aka fi sani da rashin tsoro, da juriya, da kasancewa duk wani makami ba ya tasiri a kansu sakamakon ire-iren magunguna da suke ci. 'Yan tauri su ne suka yi ruwa da tsaki wajen samar da tsaro. Sannan suna taka muhimmiyar rawa ta fuskar samar

da magungunan gargajiya na kariyar kai, (riga-kafi), da na warkar da cututtuka, da raunuka musamman waɗanda ke samuwa a yayin da ake amfani da kayan aiki da suka shafi ƙarafa. Haka nan kuma suna taka muhimmiyar rawa wajen nishaɗantar da al'umar Hausawa da kiɗa da waƙa, wanda babu wani wuri da ake ɓarje guminsu fiye da cikin al'adar Tauri.

**2.3 Ma'anar Kalmar "Farfajiya".**

Kalmar Farfajiya, kalma ce da ta ke da ma'ana mai faɗi wadda kuma ake iya danganta ta da abubuwa daban-daban. Ma'anar kalmar ita ce gurbi ko wani killataccen guri ko keɓantacce wanda aka tanda domin samun damar aiwatar da wani al'amari wanda ake buƙatar aiwatarwa. A cikin Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero Kano (2006:135, an kawo ma'anar kalmar Farfajiya da cewa: "Wani ɗan fili bayan an wuce Soro, kafin a shiga tsakar gida".

Dangane da wannan aiki na mu muna iya bayyana ma'anar wannan kalmar da iyaka, ko gurbi, ko kadada, gurbin tunanin Kassu Zurmi dangane da al'adar 'Tauri. Wannan maƙala za ta yi ƙoƙarin fito da batutuwan da za a iya samu dangane da wannan al'ada ta 'Tauri" daga cikin waƙoƙin na Kassu Zurmi..

**2.4 Ma'anar Kalmar Tunani.**

Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero, Kano (2006:444), an bayyana ma'anar kalmar Tunani da cewa: "Tara hankali wuri ɗaya don tuna abin da aka manta, ko ƙulla wani abu cikin zuciya". Wannan ma'ana ta nuna cewa kalmar tuna nufin yin amfani da zuciya ko kuma ƙwaƙwalwa, tare da tsayar da hankali wuri ɗaya domin samo, ko gano, ko fahimtar yadda wani al'amari ya ke kasancewa, tare da samuwar gaskiyar al'amarin idan ya kasance. Wato "Tunani" wani tsari ne na saƙo ma zuciya yadda wani al'amari yake faruwa a zahiri, tare da ba da damar fahimtar yadda gaskiyar al'amarin yake. Domin fahimtar yadda yanayin al'adar Tauri take ne ake ganin ya dace a ɗora ta bisa tunani Kasu Zurmi domin tantance gaskiyar al'amarin.

**3.1 Magungunan Tauri.**

Magunguna Tauri, magunguna ne waɗanda suka kasance ƙarƙashin ire-iren magungunan da Bahaushe ke samarwa domin ya samu kariya daga dukkan wani nau'i na makami, ko wata bara da wani ka iya kai masa. Dangane da waɗannan magunguna na Tauri akwai bambancin ra'ayoyi na masana. Wasu suna ganin magungunan Tauri sun tsaya ne ga makamin da aka samar daga kowane irin ƙarfe. Wasu kuma suna ganin magungunan ba su tsaya ga makami na ƙarfe kaɗai ba. Suna ganin cewa tuni Bahaushe ya samu hikimar sarrafa wasu abubuwa, kamar Kashi ko Kaho ko sayyun wasu itace ya maida su makamai. Dukansu waɗannan nau'uka ne na makamai da ake ci ma maganin Tauri. Haka nan kuma kowane daga cikin ire-iren waɗannan makamai akwai irin maganin da Bahaushe ya tanada domin samun kariya daga gare shi.

Magungunan da 'yan tauri suke samarwa sun kasau kishi biyu wato akwai na gargajiya wanda ake samar da su a gargajiyance. A cikin magungunan Tauri na Gargajiya akwai waɗanda ake samarwa ta hanyar la;akari da yanayin halittarsu da kuma waɗanda ake samu ta hanyar bautar Iskoki. A kan yi amfani da saƙe-saƙin itacen ko ganyensu ko sayu ko ɓawo ko kuma kauci. Haka kuma akwai tsirran da su ma ake amfani da ganyensu ko duka jikinsu a haɗa magungunan Tauri da su, A yayin da aka ɗebo itace ko tsirren da ake haɗa maganin Tauri ana daka su ne a mayar da su gari sannan a yi amfani da su. Ya danganta da irin yadda aka buƙaci a yi amfani da garin maganin. Ana amfani da garin magani ta hanyar sha ko wanka ko hayaƙi ko shafawa ko a tuƙa tuwo a ci. Ire-iren waɗannan nau'in garin magani, Kassu Zurmi ya jero su a cikin waƙar Na'amadu Kokirzon Kada, kamar haka:

*"Kai Hinkarin nika tambaya,*
*A'a Katakare in ka aje,*
*In ka rage **Tuƙe** 'yam mani,*
*Gandau in ba ka yi,*
*In ka rage **Kambu** 'yam mani,*
*Ka ga hwa Ancana na hwaɗa ma ni,*
*Balan gyare ka jiya,*
*In ka rage Tuƙe ci ni kai,*
*Ina na Mande, Garu-garu?*
*Ku ni ka tambaya,*
*Ko war rage **Gari** in jiya"*

Haka kuma akwai na Tsibbu, waɗanda malamai, suka samu dabarar samarwa bayan da addinin Musulunci ya shigo ƙasar Hausa. Ire-iren waɗannan magunguna na Tauri da malami ke samarwa ta hanyar tsibbu, su Kassu Zurmi yake nufi da Malami. Hakan ya fito a cikin waƙarsa ta ɗan tauri Shehu Ɓuraguji inda Kassu ke cewa:

*"Ku saha Malammai,*
*Ku ɗebi sayyu,*
*Ku yi kariya,*
*Tauri wuya gare sai da Bagaruwa,*

Cikin ire-iren magungunan Tauri, akwai waɗanda ake ɗaurawa a wani sashe na jiki da suka haɗa da Ɗamara da Kambu, da Laya da makamantan su. Ire iren waɗannan magunguna sun bayyana acikin waƙar Kassu Zurmai ta Ibrahim Shaho Bagobiri da ke cewa:

*"Kai aka wa kambuna da manyan layu,*
*Uban Tamaikiɗi,*
*Ko wac ci magani kai ya ka tsoro,*
*Iro a gama da kai lahiya ba a gamawa".*

Baya ga maganin Tauri da su 'yan taurin suke amfani da su, Kassu Zurmi ya ambaci wasu daga cikin ire-iren sauran magungunan da 'yan taurin suke amfani da su dumin ganai sun buwaya. Magungunan Buwaya wasu naukan magunguna ne waɗanda 'yan tauri, Hausawa suke amfani da su domin ganin sun gagari abokanen adawarsu. Akwai ire-iren magunguna na buwaya da 'yan tauri suke amfani da su. kuma sun kasu kishi daban-daban. Akwai waɗanda idan an yi amfani da su za a kasa dukan mutum. Akwai waɗanda mai su ba za a iya ganinsa ba. Wasu ko an ci karo da mai su ba za a iya yi masa magana ba. Kassu Zurmi ya ambaci wasu daga cikin ire-iren waɗannan magunguna da suka haɗa da:

### 3.2 Maganin Ki-bugu

Maganin Ki-bugu, magani ne wanada zai sa a kasa dukan mai irin shi. Yana danganta da ire-iren abubuwan da aka yi amfani da su wajen haɗa ko wane magani. Wani maganin zai sa idan aka zo dukan matun sai jikin wanda zai yi dukan ya yi sanyi har ya kasa ɗaga hannunsa. Wani ko makamin da aka so amfani da shi ne zai kuɓuce ya faɗi ƙasa. Ana haɗa maganin Ki-bugu a fasalin Kambu ne. Kassu ya tabbatar da cewa 'yan tauri suna amfani da maganin Ki-bugu kamar haka:

*Ko hwadama ni kai,*
*In ishe Isan ɗan Madi,*
*Su naj ji suna ƙafa,*

*Isa kai kau 'yam man **Ki-bugu,***
*In ka rage **Kambu** 'yam mani,*
*Ka ga hwa Ancana  na hwaɗa ma ni".*

**3.3 Maganin Ɓata (Ba-duhu Ko Layar Zana)**

Duk da kasancewa ana samun bambanci tsakanin layar zana da ba-duhu, a nan na game su ne domin su duka Bori ɗaya suke yi ma tsafi. Wato magunguna ne da ke sa mutun ya fake ko ya ɓace. Ya kasance duk wani mutum ko wata dababa da ka iya cuta masa ba za ta ganinsa ba. 'Yan tauri suna amfani da ire-iren waɗannan magunguna domin guje ma ɓacin rana. Da zaran ɗan tauri da yake da irin wannan magani ya samu fargaba wato faɗuwar gaba sai ya ɓata. Kassu Zurmi ya bayyana irin wannan nau'i na magani a cikin waƙar Baƙo na Ɗantsugu mai takobi karen Nagagai. A ciki yana cewa:

*"Wag ga irin magana ka sa in yi laihi,*
*Haw wasu na hwaɗin ba su so na,*
*Ga Ancana na gudu bai wuce ba,*
*Yana nan bayan duhu ba ɓace ba,*
*Sai nag ga su Baƙo na hwaskata tai*
*Naj ji yana hwaɗin kaico kai nai,*
*Ya ga Mala'ika za ta ci nai,*
*Nac ce ma shi **Ba-duhu** ba ta yi,*
*Shege tashi tcere yi gida".*

**3.4 Maganin "Ɗaurin-Baki".**

'Yan tauri musamman masu zuwa farauta sukan yi amfani da wasu magunguna waɗanda ƙarfin su zai sa, duk wani abokin gaba ba zai iya buɗa baki ya tanka ma su ba, ko da kuwa kisan kai suka aikata. Wannan kasa magana da mutun ke yi shi ake kira "Ɗaurin-baki". 'Yan tauri da ɓarayi kan yi amfani da irin wannan magani. Nan ma Kassu Zurmi ya tabbatar da haka a cikin waƙar wani Ɓarawo da ake kira Isa Ɗan Buzu. A ciki yana cewa:

*Isa na san kana da ɗaurin-baki,*
*Ko an ga Duna ba a da bakin hwaɗi".*

**3.5 Maganin Kau-da-bara**

Kau-da-bara kalmomi ne guda biyu aka haɗe wuri ɗaya, wato kaucewa wadda aka taƙaita ta koma "Kau" da kuma "Bara" wadda ke nufin farmaki. 'yan tauri su kan yi amfani da magani Kau-da-bara domin kauce wa kowane irin makami da aka so ayi amfani da shi a kansu. Kau-da-bara na nufin kaucewar da makami na jifa ko kuma harbi ka yi wa mai irin maganin. Tabbacin 'yan tauri na amfani da magungunan Kau-da-bara ya fito a cikin waƙar da Kassu ya rera ta Rabi'u Ɗanmusa. A ciki yana cewa:

*"Bari in yi ma Rabi'u kiɗa,*
*Ya tashi ya ɗebo Kau-da-bara,*
*Wadda uba nai yag gwada mai".*

**3.6 Maganin Karya-tambaya**

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

Duk lokacin da aka ambaci tambaya a irin wannan fage, ana nufin maganin da ɗan tauri yake da shi. Karya-tambaya na nufin a ɓata wa ɗan tauri irin magani ko magungunansa Kassu ya tabbatar da cewa 'yan tauri suna amfani da irin wannan magani duk dai a cikin waƙar Baƙo na Ɗantsugu mai takobi Karen Nagagai, Kamar haka:

*"Baƙo da ba a wa Kau-da-bara,*
*Wani wani ya gwada Ba-duhu bai ɓace ba,*
*Kun ga hwa Ancana ya gwada bai ɓace ba,*
*Shina nan bayan duhu bai wuce ba,*

A sakamakon haka ya sa kowane ɗan tauri ya kan tanaji magani ko wata dabara ta yadda ko da wani ya so ya ɓata masa magani ba zai iya ba. Samun irin wannan kariya daga masu nufin ɓata magani da ɗan tauri ya ke da ita na sa shi ya kasance ya buwaya.

### 3.7 Maganin Maza

'Yan tauri suna tanadar wasu magunguna na musamman domin su kare kan su daga sihirce-sihircen abokanen adawa. Ire-iren waɗannan magunguna sun haɗa da maganin kandun-baka da na Sammu da makamantansu. Wato duk ɗa namiji da ke wurin zai kasance ba namiji ba ne idan mai irin wannan maganin na wurin. Su kan tanaji ire-iren waɗannan magungunan ne domin gudun ɓacin rana, kuma su kasance sun buwaya. A cikin waƙar Iro Ɗanbaran Dila Kassu ya gargaɗi tauraron nasa da cewa ya tanaji irin wannan magani. Kassun na cewa:

*"Ku ci maganin maza,*
*Iro maza hwa ba su da daɗi,*
*Allah Ya kau da ɓacin rana,*
*Rana ta ɓatam ma Annabawa ran yaƙi bare a sansani,*
*Jama'a bare a sansani na banza"*

## 4.0 Yadda Ake Amfani Da Magungunan 'Yan tauri.

Akwai hanyoyi mabambanta da 'yan tauri ke amfani da magungunan Tauri waɗanda suka haɗa da ci ko sha ko ratayawa ko kuma su ɗaura a wani sashe na jikinsu. Kassu ya ambaci hanyoyi da ake amfani da magungunan, kamar haka:

### 4.1 Sha.

Hanyar ta farko da 'yan tauri suke amfani da mafi yawa daga cikin magungunan tauri it ace ta hanyar sha. Duk lokacin da aka haɗa maganin Tauri bayan an daka shi ya koma gari sai a riƙa ɗiba ana zuba shi cikin ruwa ko nono ka kunu ko fura da makamantansu ana sha. Wasu daga cikin magunguna ana shan su da zuma. Tabbacin ana shan maganin tauri ya fito cikin waƙar Maitawaliya da Kassu Zurmi da ya rera. Yana cewa:

*"Ku sha magani banawa,*
*Kada ƙato ya ɗauki horon uban wani".*

### 4.2 Ci.

Kamar yadda ake shan wasu magungunan haka kuma wasu ake ci da wani nau'i na abinci. Daga cikin akwa waɗanda ake tuƙa su da garin gero ko na dawa ana ci wato "Tuƙe". Akwai kuma wanda ake ci da gayan tuwu. Haka nan kuma akwai waɗanda ake ci da wainar gero ko ta dawa. Kassu Zurmi ya ba da tabbacin ana cin maganin Tauri a cikin waƙar Aikaun Rukudawa a inda yake cewa:

*"Ku ci magani ya kam ma ku alheri ya ƙare,*
*Akwai mu da baƙi Tunku mai biɗam ma dangi nai sharri"*

(Kassu Zurmi, Sa maza lumana Aikau baba Suri).

### 4.3 Ɗaurawa

Hanya ta gaba da ake amfani da maganin Tauri ita ce ta ɗaurawa a jiki. Akwai wasu magungunan Tauri da 'yan tauri ke ɗaurawa a jiki da suka haɗa Laya da ake ratayawa a wuya, sai Kambu wanda ake ɗaurawa a hannu. Akwai Kiri ko Guru da Ɗamara waɗanda ake ɗaurawa a ƙugu. A cikin waƙar Sanda na Galadi manyan hwarauta Kassu na cewa:

*Sai ka ga ƙato da Ɗamarru da Laya,*
*An tahi kasuwa Galadi,*
*Ba saye ba sayarwa,*
*An dai zo dan biɗaz zangz-zanga,*

### 5.0 Matsayin Tauri a Mahangar Kassu Zurmi

Kasancewar Kassu Zurmi mawaƙin Tauri da ya fahinmci wannan al'adar ya sa ya ke kallon Tauri ta fuskoki mabambanta kamar haka:

### 5.1 Tauri Ba Karya Ba Ne

Tun da fari dai Kassun yana ganin Tauri fa gaskiya ne ba ƙarya ba ba kuma abun banza ba ne domin kuwa yana da muhimmanci. A cikin waƙar Basare Ɗan Isiyaku Kassun ya kawo wani baiti da ya gwada hakan. Yana cewa:

*"Tauri ba ƙarya ba,*
*Ba ƙarya ne ba, yara kun ji kiɗin amsar rai".*
*"Tauri ba banza ba,*
*Ku sha malammai".*

### 5.2 Tauri Mugunyar Sana'a Ce

Ta wata fuskar kuma Kassun ya hangi Tauri a matsayin wata mugunyar sana'a ce wa ka iya sa ɗan tauri kasa zama gidansu. Ya fito da hakan a cikin waƙar Ibrahim Maishura. A ciki yana cewa:

*A'a ku bar ganin da halinku yaranku garkuwa ce,*
*Wa ka mugunyar tsirhwa,*
*Rad da za ka hwara da uba hwaɗa uwa na kuka,*
*Tana hwaɗin ka bari ba ka jin wa'azin kowa,*
*Sai waɗan ga tsaffin banza,*
*Sai kau malamin da kai ma ƙarya ga kamanta karon arna,*
*Sai mai ce daddaƙi wan ga ɗebo wan ga,*
*Ba rabon tama ga jikinka,*
*Ba ka bari sai ran da an kayo raben dan-dan-dan,*
*An yo hwaɗan zube ban kwarya,*
*Ran da kag ga aikin Tauri,*
*Ka iske ta ƙuƙe ba a son ɗabi'at tauri,*
*Wan da an ka wa ɓanna na kwance,*
*Dangi su na gadon ɗauka tai,*
*Ko ya so ya tafi gida ba dama,*
*Shi kau wanda yay yi ɓannai,*
*Sai zage-zage gidan shi zan suriki nai,*
*Ya ce ma bara nai kayana na wuri kaza,*
*Ɗauko mani ina wuri kaza iske ni,*
*A! Ka ji ta ƙunƙe ba a son ɗabiat tauri.*

(Kassu Zurmi, Iro na Labbo ɗan namiji duniya na malan Ɗanja).

**5.3 Tauri Ya Ɓaci.**

Ta wata fuskar kuma Kassu Zurmi ya hangi cewa a lokacinsu Tauri ya ɓace. A nan yana nuni da cewa 'yan zamani sun ɓata harkar Tauri. A cikin waƙar Labbo Na'amadu Kassun ya tabbatar hakan tare da kawo dalilansa na wannan hasashe da ya yi, kamar yadda ya ke cewa:

*"Jama'a Tauri yanzu sun ɓata shi,*
*Su sun ka maisam wasa,*
*Tauri kau ba bananci na ba,*
*Tun da irin na zarumci ne,*
*Sun mai da Tauri wasa,*
*'Yan tauri sunka maisai ɓanna,*
*Ka ga ƙato kwasham da takobi,*
*Rima da ɗamarru,*
*An tahi Kassuwa da ɗamarru,*
*"Abun ga an yi kau dan daji,*
*Kuma ba Kassuwa aka ci ba,*
*Sai a wuce gidan karuwwai,*
*Za ni ganin uwaɗ ɗakina,*
*Da gani nai ita kau ta zaburo,*
*Ka ji ta ce maraba da yaya,*
*Shi ya ce uwaɗ ɗakina,*
*Ita kau ta ce maraba da yaya,*
*Nan muka gane abun muhucci ne,*
*Dan nan sai kamun gida da ɗamarru,*
*Ga kayanmu nan ki aje mamu sai mun dawo".*

**5.4 Tauri Abu Ne Mai Wuya**

A cikin waƙar Shehu ɓuraguji kuwa sai Kassun ya nuna cewa tauri fa wuya gare shi kamar haka:

*"Ku sha malammai ku ɗebi sayyu, ku yi kariya,*
*Tauri wuya ga rai sai da Bagaruwa,*
*In ko an ƙiya ana cim ma sanin wani".*

(Kassu Zurmi, Mai Babarbar Shehu Ɓuraguji)

Amma a ckin waƙar na gidan Duwa kuwa sai Kassun ya ke nuna cewa fa tauri na kautata ma masu shi, a yayin da ke cewa:

*Ku sha magani kwarai dan Allah ku biɗi kariya,*
*Ku waɗanda sarki ka kira ga mugun wuri,*

(Kassu Zurmi, waƙar Iro Raƙumi Gujiya).

**6.0 Kalmomi da Kassu Zurmi ya yi amfani da Su da A Mamadin Magungunan Tauri.**

A cikin waƙoƙin Kassu Zurmi na Tauri akwai waɗansu kalmomi da ya yi amfani da su a mamadin maganin. Ba a yi ƙasa a guiwa ba wajen tabbatar da ganin an lalubo waɗannan kalomomi. An yi hakan ganain cewa akwai bukatar a gabatar da su a cikin wannan maƙala domin a tabbatar an yi ma turakun Tauri feɗar biri har wutsiya. Daga cikin kalmomin da Kassu Zurmi ya yi amfani da su a mamadin "Magani" akwai:

**6.1 Tambaya.**

Bisa ga al'ada, ba kasafe 'yan tauri ke bayar da irin maganin da suke da shi ba, ba tare da wanda ke bukatar wannan magani ya tambaya ba. A irin wannan hali mai bukatar magani zai fahimci cewa, wane yana da wani nau'in magani da ya ke sha'awar samun irinsa. Daga nan sai ya tafi ya tambayi mai maganin. Ganin ba a samun magani sai an tambaya ne ya sa Wato an faɗaɗa ma'anar kalmar har ake kiran maganin da suna 'Tambaya'. Ida nana batun maganin Tauri z ace ai wane yana da tamabaya ko ya samu tambaya. Wato yana da magani ke nan. A cikin waƙar Na'amadu Kokirzon Kada, Kassu Zurmi ya yi amfani da kalmar inda yake nufin 'yan tauri su duƙufa wajen ƙara yin magani. Kassun na cewa:

*"Ku yi **Tambaya'***
*'Yan tauri ku yi **tambaya,***
*Na'amadu na nan na ta yi".*

**6.2 Biɗa:**

Wata kalma da ake kiran maganin Tauri da ita ce 'Biɗa'. Kalmar biɗa tana nufin nema, misali mutum ya tafi neman wani abu wanda yake bukata ganin ya samo shi. A al'adar Bahaushe, musamman 'yan tauri suna gani baka samun magani a gida, dole sai ka fita wajen wasu. Ko da kuwa ya kasance akwai na gida wanda aka gada kaka da kakanni, to akwai bukatar a ƙara da irin na wasu. A irin wannan hali mai son ya samu wani nau'i na magani daga wurin wasu ya kan tafi ya zauna warin mai irin wannan magani ya yi barantaka ta tsawon lokaci, har sai ya samu maganin kana ya komo gida. Abin nufi shi ne an fita an biɗo magani, mamadin a kira wannan maganin biɗaɗɗe sai ake kiransa 'Biɗa'. Basare ɗan Isiyaku ya yi amfani da wannan kalmar a cikin kirarinsa, lokacin da Kassu Zurmi key i masa waƙa. Yana cewa:

*"Ku yi **biɗa** ga dattiɓayya,*
*Akwai magani ga dattiɓai,*
*Ko wab bi ta dattijo ba ya kunya daji".*

(Kirarin Basare ɗan Isiyaku a cikin waƙar Kassu Zurmi).

**6,3 Asiri.**

Kalmar asiri, kalma ce wadda ta ke nufin sayawa, ko rufewa, ko ɓoyewa domin kada wani abu ya bayyana. Tun asali al'amarin magani ya zama abun ɓoyo ga Bahashe. Babu wani ɗan tauri wanda ke son a san irin hanyar da yake bi yana samar da irin maganin da ya ke da shi. Domin gudun kar wani ya yi masa kutse a cikin wannan harkar, ko ma ya kasance an san hanyar da za a bi a ɓata masa irin maganin da ya mallaka. Wannan ya sa sai ya ɓoye abinsa. Haka kuma ba kasafe duk wani mai magani ke son a sani ya mallaki magani, ya fi so sai lokacin da bukata ko amfanin wannan magani ya taso, wato lokacin da rana ta ɓace sannan a gane yana da maganin. Sakamakon bukatar ɓoye irin waɗannan magunguna ne ya sa ake kiransu da wannan Kalmar ta 'Asiri'. Kassu ya yi amfani da kalmaar 'Asiri' cikin waƙar Ibrahim Shaho Bagobiri. Yan a cewa:

*"Kura ta riga Kare kai ga asirrai na Jibir,*
*Kai kau ka riga su ka shanye makammai".*

**6.4 Shiri.**

Kalmar shiri ta samo asali daga shiryawa wadda ke nufin mutum ya yi tanajin samun sauƙin gudanar da wata manufa ta sa. Yin tanajin wasu magunguna na kariya da ɗan tauri ke yi domin gudun ɓacin rana shi ne ake kira 'Shiri'. Tabbacin kiran ire-iren waɗannan magunguna da 'yan tauri ke da su ya fito ƙarara a cikin waƙar Musa na ƙasar Ɗan'ali wadda Kassu Zurmi ya rera. A ɗaya daga cikin ɗiyan waƙar yana cewa:

*"Tsoho bai ta da kai nai ba,*
*Bai ko kau da kai nai ba,*
*Sai yai ta jiƙon ɗarairai nai,*

*Ya san ya **shirya** yara nai".*

**6.5 Kariya.**

Wani sunan da 'yan tauri ke kiran irin magungunansu shi ne Kariya. Wato ya zama mutum yana da magani wanda a tunaninsa shi ne zai kare daga duk wani makami da za a iya far masa da shi. Irin wannan samun kariyar shi ne suka laƙaba ma sunan magungunan. Misalin irin wannan suna da ake kiran waɗannan magungunan ya fifo, shi ma a cikin waƙar Kassu Zurmi wadda ya rera ta Shehu Ɓuraguji. Acikin waƙar yana cewa:

*"Sai ku sha malami,*
*Ku ɗebi sayyu ku yi **kariya,***
*Tauri wuya garai sai da Bagaruwa".*

**6.6 Sani.**

A cikin ɗango na ƙarshe na cikin wannan baitin Kassu ya kawo wata kalmar, wato "Sani" wadda ake amfani da ita a matsayin magani. A nan 'yan tauri suna danganta ilmin da suke da shi na sani ko fahimtar magunguna daban-daban da suke amfani da su. A cikin wannan ɗan waƙa da Kassu ya kawo yana nufin maganin da wani ya sani, ya kuma yi amfani da shi.

*"Tauri wuya garai sai da Bagaruwa,*
*In ko kun ƙiya kuna cim ma **sanin** wani,*
*Kassu iana ruwanmu tunda ba ni ka gama ku ba".*
(Kassu Zurmi, Mai Babarbara Shehu Ɓuraguji)

**6.7 Roƙaƙƙe.**

Duk yadda ɗan tauri ya kasance yan da magani ko da kuwa gadon abunsa yay i taozai bukaci ya ƙara da irin na wasu dan haka sai ya tafi wurin wannan mai magani ya roƙe shi. Idan mai son maganin nan ya ci sa'a aka ba shi maganin a sakamakon roƙon da ya yi, shi ne ake cewa ya roƙo magani. Haka nan kuma bayan wani lokaci magain yana iya ƙarewa tun da ba gidansu tushen maganin ya ke ba. Maganin Tauri da aka roƙo shine Kassu yake kira 'Roƙaƙe'. Haka nan kuma ba tushe ko gidin maganin aka ba shi ba, bare idan ya ƙare ya tafi ya ɗebo da kansa ba. Yana cewa;

*"Kai mai **roƙaƙƙe** ko ya ƙare?*
*Daji waɗanda sun ka gad aka walkami ciki,*
*Hwaɗa shina ga mai magani kwarai,*
*Kada yaro ya ɗauki horon uban wani,*
*Ka ya ce ana ba shi gaskiya Ɗandarman,*
*Daji waɗanda sun ka gada ka walkami ciki,*
(Kassu Zurmi, waƙar Turbe ɗan Dattawa mai maganin maza).

**7.0 Shawara**

Kafin gabatar da shawarwarin da ake ganin sun dace, akwai buƙatar tunatar da mu irin halin da muka tsinci kawunan mu a ciki. Wannan hali kuwa shine na rashin tsaro da hirgici a ƙasar nan musamman ma a jihohin da Allah ya albarkace ta da duka mazajen da Alhaaji Abubakar Kassu Zurmi ya garzaza. Waɗanna zaruman 'yan tauri sun taka muhimmiyar rawa wajen ganin wannan ɓangare namu ya samu kyakkyawan tsaro a lokacin rayuwarsu. Da kuma irin sakacin da aka yi na kasancewa juyin zamani yanyi tasiri ga al'adunmu. A tunanina da za a koma a riƙa nazartar waƙoƙin da mawaƙa irin su Kassu Zurmi suka rera da yadda suka riƙa ba da shawarwari domin gani zamantakewar al'umar Hausawa ta samu tagomashi da har a samu ci gaba. Dangane da harkar samar da tsaro da irin hasashen da Kassu Zurmi ya yi kafin fakuwarsa ya ba da shawarari kamar haka:

- Daga cikin shawarwarin da Kassu Zurmi ya ba da, ta farko ita wadda yake jan hankali ga al'umar da cewa su miƙe su duƙufa yin tambaya domin samun magungunan da za su yi amfani da su domin ganin sun samu kariyar jikunnan su. A hasashen Kassu Zurmi na rashin kwanciyar hankali a duniya bai kau ba. Wannan ne ya sa ya ke gargaɗin jama'a da su ƙara shiri. Ya fito da wannan buƙata tasa a cikin waƙar da ya rera wa Sanda Bagobiri. Yana cewa:

  *"Ku koma shiri,*
  *Duniyag ga hay yanzu da yamutci,*
  *Duniyag ga hay yau bata gyaru ba".*

- Wata shawara da Kassu ya bayar ita ce ta tunatar da al'umar Hausawa cewa fa babu alheri ga irin zaman da ake ciki a wannan ƙasar tun zanin yana raye. Dan haka yake ba da shawar cewa jama'a su sha magani da gaske domin samun mafita ga irin halin rashin alherin da ake ciki. Ya gwada cewa a ƙasar nan akwai bakin Tunku da kea biɗar ma dangi wahala. Ya kawo wannan batu a cikin wani baiti na waƙar Aikau na Rukudawa wadda ya ke cewa "Sa maza lumana Aikau baban Suri". Kassun yana cewa:

  *"Ku ci magani ya kai maku alheri ya ƙare,*
  *Tunda akwai mu da baƙin Tunku,*
  *Mai biɗam ma dangi wahala".*

- A wani ƙaulin kuwa sai Kassu Zurmi ya gwada cewa a ƙasar Hausa fa akwai 'yan uba waɗanda kullun suke ƙoƙarin ganai sun takaita al'uamr Hausawa. Dominhaka ne a cikin waƙar Bala Gumi yake ba da shawara da a ƙara neman magani domin ganin an kawar da ire-iren waɗannan 'yan uba. A cikin waƙar yana cewa:

  *"Bala ƙara magani,*
  *A dai ƙara magani,*
  *Tunda akwai mu da yaƙi da 'yan uba".*

- Shawara ta gaba ita ce wadda Kassun ya bayar wadda kuma take da muhimmanci ga al'uma ita ce wadda ya ke cewa a yi ƙoƙari a kwace dukkan makamai da Turawa suka shigo da su ƙasar nan. A ciki Gora Namagaji Haki Tsaurin Kasa. Yana cewa:

  *"Ku amshe makammanku Turawa,*
  *Ku amshe makammai Turawa,*
  *Amma dai a tsaya ga hwaɗan Gargajiya,*
  *Dan wani ka ya sharara man wuta".*

**Naɗewa.**

Allah Ya albarkaci ƙasar Hausa da shahararrun mawaƙa waɗanda Allah Ya ba su hikima da fasta ta sarraf harshe da tunani. Abubakar Kassu Zurmi na daga cikin ire-iren waɗannan mawaƙa. Ya kan yi afani da fasaharsa wajen gina waƙoƙinsa. Kamar yadda muka gani a cikin wannan maƙalar ya kawo fasalin magungunan Tauri da yadda ake sarrafa su da yadda ake amfani da su. Ire-iren waɗannan turakun waƙoƙi suna kasancewa a matsayin Hannunka-mai-sanda ne tare da kasancewa wata taska ta adana al'adun Hausawa musamman waɗanda suka shafi al'adar Tauri. Akwai fannoni daban-daban da ya ɗauka ya gina turakun waƙokinsa waɗanda suke bukatar a binciko tare da nazartar su domin adanawa.

**Manazarta**

Atuwo, A. A. (2016). "Tsiya Adon 'Yan Tauri: Nazarin Ayukkan Kungiyoyin Banga ga Tsaron Kasa a Wasu Sassan Adabin Hausa". Dagel Journal of Faculty of Arts and Islamic Studies, Vol. 13, (December, 2016).

Bunza, A. M. (1990) *"Hayaƙi Fid da na Kogo"* (Nazarin siddabaru da sirrin Hausawa) Kundin Digiri M. A. Jami'ar Bayero, Kano.

Bunza, A. M. (1995) "Magani a Rubuce," Kundin Digirin Ph. D. Jami'ar Bayero, Kano.

Buza, A. M. (2001). "Kamanci da kwatanci Cikin Asirin Tsibbu". Hausa Studies. Reading In Hausa Languege, Litreture and Culture. vol. III, N0. 3. Department of Nigerian Languages, Universiyt of Sokoto.

Bunza, A. M. (2006), *Gadon Feɗe Al'ada*, Tiwal Nigeria Ltd.

Bunza, A. M. (2009) *Nazarin Adabin Hausa.* Kaduna Fisbas media Service

Gobir, Y.A. (2002). "Tasirin Iskoki ga Cutuka da Magungunan Hausawa" Kundin Digiri na Uku. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Gusau, S. M. (1996) *Makaɗa Da Mawaƙan Hausa.* Kaduna: Fisbas Media Service.

Gusau, S. M. (2003) *Jagoran Nazarin Waƙar Baka.* Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S. M. (2008) *Waƙoƙin Baka A Kasar Hausa Da Yanaye-yanayensu.* Benchmark Publishers Limited, Kano- Nigeria.

Gusau, B. M & Gusau, S. M, (2012) *Gusau Ta Malam Sambo.* Benchmark Publishers Limited.

Gusau M. M. 2018. *ZAMFARA.* Jihar Da Aka Manta Da Ita A Tarihin Nijeriya.

Gusau, S. M. *Dangantakar Waƙoƙin Baka da Al'adun Hausawa: Bunƙasa ko Koma-baya.* A paper presented at the International Comferance, Katsina Nigeria: Umaru Musa 'Yar'adua University and Katsina History and Culture Bureau. *KATSINA STATE HISTORICAL GUIDE II (1997).* Produced By Katsina State History and Cultuer bureau, Katsin.

Iguda, S. (2022). "Asalin Tsibbu A Tsangayun Alƙur'ani". Googleweblight.com.ng

Lawal, A da Tafida, A. M. (1987) Magungunan Gargajiya da na Turawa. Dangantakarsu da Bambance-bambancensu da kuma Tasirin Magungunan Turawa a kan na Al'ummar Hausawa Kundin Digirin B. A. Jami'ar Sakkwato.

Sallau, B. S. (2009). "San'ar Wanzanci da Sauye-sauyen Zamani". Kundin Digiri na Uku. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Sallau, B. S. (2010) *Wanzanci Da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* M.A. Najiu Professional Printers. No. 3, Kenya Road Malali Kaduna.

Sayaya, A.S. (2009) Wasan Tauri A Kasar Katsina. Kundin Digirin M.A. Jami'ar Usmanu Ɗan Fodiyo, Sokoto.

Sayaya, A. S. (2013) Gudummuwar Farauta Ga Raya Al'adar Bahaushe". *Excerpts of International Seminar On The Deterioration Of Hausa Culture.* Organised by Katsina State History And Culture Bureau Collaburation With Umaru Musa 'Yar'aduwa University, Katsina.

**Muatanen da aka tuntuɓa**

A ƙoƙarin tattaro bayanen da na samu a kan waƙoƙin Alhaji Abubakar Kassu Zurmi na samu tattaunawa da wasu mutane a lokutta mabambanta da suka haɗa da:

1. Ibrahim Gurgu Jabanda
2. Muktar Jikan Baƙo na Ɗantsugu Mai Takobi
3. Alhaji Manade Zurmi.
4. Nazuru Sarki Dogaran Sarkin Zamfaran Zurmi
5. Alhaji Goje Kofar Kaura
6. Malam Amadu Na Amadu Goran-namaye

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 